# Yabo a Bakin Zabiyar Fada

**Halima Kabir Daura,**

**Gabatarwa**

Masu iya magana na cewa, "Yaba kyauta tukwici". Tukwicin da mawaƙa ke yi wa jama'ar da suke ba su abin hannunsu shi ne ta hanyar ambato abubuwa na gari a cikin waƙoƙinsu ko kirari. A iya cewa Zabiyoyin Fada kamar takwarorinsu maza, ba su yi butulci ba, su ma suna okari wajen yabon saraki da shikashikan cim ma yabo, waɗanda suka haɗa da : ambaton tarihin asali ga sarauta, da riƙo da addini, da kyauta, da jaruntaka, da kuma iya mulki ko riƙe jama'a, kamar yadda Bello (1976), ya bayyana. Amfani da yabo a matsayin jigo, musamman a waƙoki da kirarin fada, ruwan dare ne, domin shi ke ƙara wa saraki kwarjini da ƙima, a idanun talakawansa da sauran jama'a, baya ga sa saraki tunƙaho.Wannan muƙala ta yi ƙoƙarin bibiyar yabo a kirarin da Zabiyoyin Fada kan aiwatar a wasu fadojin ƙasar Hausa.

Kalmomin Fannu: *yabo, fada, zabiyar fada.*

**2.0Yabo**

Masana irin su Bello (1976), da Ibrahim (1983), da Furniss (1996), da Diso (1997), da Tsoho (2002), da Gusau (2008), sun yi tsokaci a kan *yabo*kamar haka:

"Yabo shi ne faɗin abubuwa na gari game da mutum, abubuwan da idan an ji su, za a so shi ko a ƙara ganin girmansa. Waɗannan kalamai na abubuwan alheri, suna cikin abubuwan da makaɗan sarauta suka fi ƙarfafawa" (Bello,1976:24).Shi kuwa Diso (1997), ya bayyana yabo ne da ƙoƙarin ɗaukaka daraja, ko ƙimar mutum ko wani abu a idon mutane ta hanyar faɗar kyawawan maganganu game da shi, yadda duk wanda ya ji waɗannan maganganu, zai ji yana ƙaunar wannan mutum ko bin zuciyarsa. A kuma ra'ayin Kafin Hausa (1997:100), yabo tamkar a sa sabulu ne a wanke mutum tas ta hanyar faɗin duk kyawawan halayensa, masali, halayen bajinta da kwarjini da martaba waɗanda Allah ya ba shi. A yayin da Gusau (2008:461), ya bayyana yabo a matsayin ambaton kalmomin sambarka da nufin nuna amincewa da hali ko wani abin da mutum ya yi na gari, ko wani lafazi da ake yi ga mutum domin a nuna halayensa abun ƙauna ne. A taƙaice, a iya cewa yabo furuci ko maganganu ne na godiya ta hanyar fito da wani domin sauran jama'a su san shi, su san ƙimarsa da darajarsa, su kuma ƙaunace shi. Yabo na daga cikin manyan turakun da makaɗan baka suka fi yawaita yin waƙoƙinsu a kansu. Kusan shi ne ma fitaccen tarken waƙoƙin Hausa, musamman waƙoƙin fada, domin mafi yawansu munufarsu kan kasance yabon wanda aka yi waƙa ko kirari dominsa.

**3.0 Fada**

Manyan Kamusoshin Hausa, waɗanda suka haɗa da *Bargery*(1934), da *Abraham* (1962), da *Kamusun Hausa na Bayero* (2006), da kuma *Newman* (2007), duk sun bayyana fada da 'majalisar Sarki da gidansa da ma kewayensa'. A yayin da Mazawaje (1985:1), ya bayyana fada da wurin zartar da hukunci. Kamar kuma yadda Hauwa (2008:66-67), ta yi ƙarin bayani da cewa, fada wuri ne na gudanar da mulki, inda Sarki yake shugaban majalisa, sai Waziri, da sauran manyan mutane masu riƙe da muƙamai daban-daban, waɗanda suka haɗu suka kafa majalisar zartarwa. A taƙaice, a iya cewa 'fada haraba ce ta mulkin Sarki a duk inda yake, kuma nan ne

muhallinsa ko tushen masarauta. Fada wuri ne na ba da umarni, saboda haka, ba gini ne fada ba, ko gari ko birni, ko daji Sarki ya sauka, to nan ma fada ce, domin nan ma za a iya zartar da hukunci da kafa aƙida. To, haka kuma, fada na ɗaukar ma'anar samun shiga, masamman ga wani babba.

## 4.0 Zabiyar Fada

*Bargery* (1934), da *Abrahams* (1962), da *Kamusun Hausa* (2006) duk sun bayyana 'zabiya' da 'matar da kan jagoranci waƙa', a yayin da Kamusun Hausa, ya bayar da ma'ana ta biyu da: 'matar da a kan ajiye a fada domin yi wa Sarki da sauran masu sarauta kirari'. Wannan ma'ana ta biyu, ita ta yi daidai da 'Zabiyar' da wannan bincike yake nufi. Saboda haka, idan ya ambaci 'zabiya', ita ake magana a kai. Zabiya tana ɗaya daga cikin maroƙan sarauta a Kasar Hausa, kuma kamar sauran makaɗan sarauta, da sukan gaji kiɗa na sarauta, to haka ma Zabiyoyin Fada, yawancinsu sun gaji Zabiyanci ne daga iyaye. Kodayake sauyin zamani ya sa waɗansu sun yi haye, musamman saboda albashin da ake biyan Zabiyoyin Fada a yau, saɓanin da, lokacin da hasafi kaɗai ake yi masu.Aikin Zabiya na musamman a fada shi ne yi wa saraki kirari, wato Sarki da matansa da 'ya`yansa da hakiman yanka, musamman a da, da ba a ba kowa sarauta a Kasar Hausa sai ɗan-na-gada. Babban aikin Zabiya shi ne fito da Sarki fada daga cikin gida duk safiya, tana gaba, tawagar Sarki na bayanta, tana yi masa kirari. Bayan da aka kammala zaman majalisa kuma, tana mayar da shi gida, cikin kirarinta. Ita ke sanar da fadawan waje fitowar Sarki, ita kuma take sanar da mutanen gida dawowarsa, a nan a iya cewa 'kirarin nata yana matsayin 'sanarwa' da gaisuwa ga saraki. Wannan kirari da Zabiyar Fada kan aiwatar shi ne Zabiyanci. Kirarin Zabiya, yana kwarzanta Sarki da ƙara masa ƙima da martaba, da kwarjini da ƙara tabbata da matsayinsa da mutuncinsa, musamman a idon talakawansa. Yana kuma ƙara sa saraki ya ji babu kamarsa, baya ga nishaɗantar da sauran jama'a. A da can da ake yaƙe-yaƙe a Kasar Hausa, da zabiya ake tafiya filin daga, domin kwarzanta maza, su sami ƙarfin gwiwar fatattakar abokanan gaba, a ci nasara a kansu. Idan kuma ba a tafi da ita ba, tana rakiya bayan gari, ta kuma tarbi mayaƙa lokacin da suka dawo.

## 5.0 Yabo a Bakin Zabiyar Fada

Bello, (1976:26), ya bayyana cewa mawaƙan fada suna ɗora yabo a kan shikashikan cim ma yabo biyar da suka haɗa da jaddada addini da asali, haɗe da ambaton zuri'a, da jaruntaka wajen yaƙi da iya mulki da kuma kyauta. Masanin ya jaddada cewa waɗannan shikashikai, suke ƙara nuna dangantakar makaɗi da ubangidansa, su kuma razana abokanan hamayya, baya ga ƙarawa Sarakuna ƙarfin gwiwa da faranta masu rai, su ƙara shaƙatawa, su yi abin da suke so.Zabiyoyin Fada a ƙasar Hausa, a yayin aiwatar da kirarin da suke yi wa saraki ba su yi ƙasa a gwiwa ba wajen amfani da waɗannan sinadarai na cim ma yabo.

## 5.1 Tarihin Asali

Asali na iya ɗaukar ma'anar 'mafari', ko'tushe', ko kuma 'salsala'. Asali kamar yadda ma'anarsa ta nuna, asalin mutum shi ne tushensu ko salsalarsa. Asali idan na gari ne, abin tunƙaho ne, musamman ma a ce na sarauta ne ga saraki. Haka ya sa ga duk wanda ya san yana da asali na fadi, yake alfahari da shi, yake jin daɗi a faɗi a gaban kowa, ba tare da tababa ba. Wannan ya sa mawaƙan fada, a kullum suke ƙara jaddada tarihin asalin saraki, na sarautar gidansu, ba ga shi kansa kawai ba, har ma da sauran jama'a, musamman abokanan hamayya, domin a razana su. Alalmisali, basaraken ɗan wane ne jikan wane. Ana kuwa danganta shi da magabatansa ne waɗanda duniya ta sansu, domin a nuna salsalarsa ga sarauta, ta hanyar gado, wanda ke nuni da

cewa, sarauta ba hayenta ya yi ba. Masu iya magana dai sun ce, "Sanin asali ya sa kare cin alli". Galibi, a sha'anin sarauta, ba a son mai gajeran asali, wato wanda yake a sarautar haye ya yi, ba gadonta ya yi ba. Saboda haka, makaɗan fada a kodayaushe ƙoƙarinsu shi ne su nuna cewa shi basarake, sarauta da ma abin sa ce, 'ɗan na gada ne', wanda ya fi 'ɗan na koya'. To, haka kuma, sun fi jin daɗin yi wa basaraken da ya gaji iyaye da kakanninsa waƙa ko kirari, saboda sun fi samun abubuwan da za su faɗa game da nasabarsa.

To haka kuma, idan muka koma ga kirarin Zabiyar Sarkin Daura (Dakamar Sarkin Daura), za mu ga wannan nuni na dangantaka ta salsala ga Sarkin Daura ya fito, a inda take cewa:

*Zabiya: Hawan 'yan Bawo,*

*`Yan amshi:* Hawan 'yan Bawo,

*Zabiya: Kakan anna,*

*`Yan amshi: Kakan anna,*

*Zabiya: Hazo na Muhamman,*

*`Yan amshi: Hazo na Muhamman… (Kirarin Sarki Daura).*

Kamar yadda tarihi ya nuna, Bawo ya yi sarautar Daura, saboda haka, wannan matani na Zabiyar Daura, na nuni da asalin Sarki daga kakansa Bawo, har zuwa ga iyayensa, har sarauta ta kawo kansa. Watau gado ya yi na Sarautar Daura, ba haye ya yi ba. Ta kuma yi amfani da 'hazo' ne, domin ta nuna tushen Sarki, daga Muhamman Bawo. A iya cewa sarakin Daura, a kodayaushe suna tunƙaho da asalinsu na 'Bawo', domin zuri'arsa ke mulki har yau, in ban da jihadin Shehu Usman Danfodiyo da ya fatattake su, suka yi hijira har na shekara ɗari, (100), amma, sarautar ta dawo hannunsu.

Idan kuma muka koma ga nazarin kirarin Zabiyar Haɗeja, irin kirarin da take yi wa sarakin Haɗeja, an ce an tsinci dame ne a kala, ko kuma a ce dodo ɗaya ake yi wa tsafi, domin ita ma a kullum tana ƙoƙarin fito ko nuna asalin saraki ne a kirarinta. A iya cewa, ita ɓaro-ɓaro, ko a kai tsaye take nuna wannan salsalar, domin tana yawan ambaton matanin da ke tabbatar da cewa a sarauta, ɗan na gada ya fi ɗan na koya, a kirarin mafi yawan sarakin Haɗeja, in ban da na Mai Martaba Sarki, misali a kirarin Ɗan Buran Haɗeja tana cewa:

*…Kai ne Mabuɗi Muhammadu,*

*Ɗan na gada wanda ya fi ɗan na koya …(*Kirarin Ɗan Buran Haɗeja).

Zabiyar Haɗeja, a kirarin Sarki, tana nuna salsalarsa ko tushensa kamar haka:

*Kai ne Buhari kai ne Sambo,*

*Kai ne gagara gammo da Sarki Jatau,*

*Ya gaji gadon Hari da Haru,*

*Ya mayar da gadon Sarki Kadir,*

*Ya mayar da gadon Sarki Karamba…(Kirarin Sarkin Haɗeja).*

Sarki Buhari da Sarki Sambo da Sarki Hari, da ma Sarki Haru, da Sarki Ƙadir, da kuma Sarki Karamba, dukkansu Sarakunan Haɗeja ne na da. A nan Zabiyar Haɗeja, ta ambato su ne domin ta jaddada tushen Sarkin da ke kan gadon sarauta, domin dukkansu, daga uba ga Sarki, sai kaka, da kakan uba da kakan-kaka. Watau, ya gaji sarauta ne daga iyaye da kakanni, ba haye ya yi ba, da ma sarautar ta gidansu ce, idan aka yi la'akari da waɗannan Sarakuna da ta zayyano.A iya cewa wannan duk yana nuna asalin saraki ne, wanda yake ƙara jaddada cewa sarauta ba hayenta ta yi ba, a'a ita da haife shi.

Haka yake idan muka leƙa Fadar Kazaure, tatsuniyar ba ta wuce ta, 'gizo da ƙoƙi' ba, domin Zabiyar Kazaure, Hajiya Indo `Yarsukola, kasancewarta Zabiyar Sarakuna uku, watau Sarki Ibrahim Adamu, da ƙaninsa Sarki Hussaini Adamu, da kuma Sarki na yanzu, Sarki Najib Hussaini Adamu, a wasu lokuta, kafin ta yi wa Sarki Najib kirari, sai ta fara da na iyayensa. A kuma kirarin Sarki Najib, takan jaddada dangantakarta da sarautar Kazaure, daga iyayensa, kamar haka:

*Sarki Magajin Sarki,*

*Sarki Magajin Sarki Ibrahim,*

*Sarki Magajin Sarki Hussaini Adamu…(Kirarin Sarkin Kazaure, Najib Hussain Adamu).*

A taƙaice, ta danganta asalin Sarki Najib da magabatansa, waɗanda suke tsatso ɗaya, wan mahaifinsa (Sarki Ibrahim), da mahaifinsa, (Sarki Hussaini), wanda yake nuni a sasari, ba hayen sarauta ya yi ba, ɗan na gada ne, domin kakansa ma, Sarkin Kazaure Alhaji Adamu ya riƙe Sarautar Kazaure tsakanin 1941- 1968, wanda shi ma ya gaji sarautar ne daga ɗanuwansa Sarki Umaru (1922 – 1940).

### 5.2 Riƙo da Addini da Jaddada Shi

Addini hanya ce ta bauta wa ubangiji. Sarakuna a Ƙasar Hausa a wannan lokaci Musulmi ne, watau suna bin tafarkin addinin Musulunci, domin haka, kirarin Zabiyoyin Fadar Ƙasar Hausa, a kodayaushe, yabon Sarakuna yake da alaƙa da batun riƙe addinin Musulunci, da tabbatar da shi, a masarautunsu, Sarakuna suna tabbatar da addinin ne ta hanyar kare martaba da muhibbarsa, da zama abin koyi ga hukunce - hukuncen Allah. Ga abin da Zabiyar Kabin Argungu take cewa ga Sarki Muhammadu Kanta:

*Zullufi – wullufi yawanyin alaihin…,*

*Sidi mai taimako da na Allah…,*

*Yau a duniya kowa ya kwana lafiya,*

*Ya tashi lafiya yakan yi miƙa,*

*Ya yi tasalimi ya tambayi alƙur'ani,*

*A kawo masa ya yi alwalla,*

*Ya mayar da gabansa gabas,*

*Ya ce ni wane na gode Allah,*

*Na gode wa Muhammadu rasulillahi…(Kirarin Sarki Kanta).*

A nan, Zabiyar ta siffanta Sarki Muhammadu Kanta, ‘mai taushin hali kuma mai tausasawa (Zullufi Wullifi), mai taimakon talakawansa saboda Allah, mai godiya ga Allah, mai kuma ibada, musamman wajen yin salla da karatun Alƙur’ani da yawaita salatin Manzon tsira, Annabi Muhammad, Salallahu Alaihim Wassalam. Wannan, ya tabbatar da cewa Sarki Kanta yana da ilimi, ilimin kuma na addinin, watau ba jahili ba ne. Sarki a ƙasarsa shugaba ne na al’umma kuma jagora na addini.

Shi ma Sarkin Zazzau, a kirarin da Zabiyar Zazzau ke yi masa, tana faɗin haka:

*Taka da ƙarfin Allah toya matsafa,*

*Fito da ƙarfin Allah toya matsafa…*

*Barka da zuwa toya matsafa,*

*Barka da zuwa duddugen addini…(Kirarin Sarkin Zazzau).*

Wannan yana nuni ga Sarkin Zazzau, cewa basaraken ya shahara ga hana ayyukan ɓarna a masarautarsa, musamman kamar yadda addini ya yi hani da su, kuma a tsaye yake wajen tabbatar da duk hukunce-hukuncen addini a masarautarsa, wato mai jaddada addini ne, kuma mai hani ne ga duk abin da ya saɓawa Islama, kamar ƙona ‘matsafa’, inda ake ‘tsafi’, da makamantansu. Watau a tsaye yake kan tabbatar da addinin al’ummarsa, shi ya sa ma Zabiyar ta siffanta shi da ‘duddugen addini’.

Akwai kuma inda kirarin ke cewa:

*Taka da ƙarfin Allah…(*Kirarin Sarkin Zazzau Shehu Idris).

Wanda ke nuni da cewa, Sarkin Zazzau Shehu Idris, basarake ne da ya yi imani da ikon Allah da buwayarsa, saboda riƙon addini. Baya ga haka, ‘Toya matsafa’, `yabau ne na aikatau” Kamar yadda Tsoho (2002), ya bayyana, yabau aikatau sunaye ne da suke nuna irin ayyuka da wanda ake yabo ya yi.

**5.3 Jaruntaka**

Jarunta ma na ɗaya daga cikin ginshiƙan da makaɗa, musamman na fada, suke ɗora yabo a kansa. Gusau (2008:387), ya bayyana ‘jarunta ’ da halin nuna juriya ko ƙarfin hali, ko bajinta (ta ƙarfi), a yayin aiwatar da wani abu. Wanda kuwa aka same shi da wannan hali shi ne ‘jarumi’, ko kuma ‘gwarzo’ (gwarzon namiji). A da can a Kasar Hausa, ana hawan gadon sarauta ne sakamakon nuna bajinta ta jaruntaka, kafin sarauta ta koma ta fuskar addini (watau lokacin masu jihadi, daga baya kuma ta koma ta gado). Tarihi ya tabbatar da cewa, an taɓa zamani a Kasar Hausa, da idan sarauta ta faɗi, ko Sarki ya yi murabus, jarumai kan fito a fafata, a nemi sarautar, ta hanyar kokawa. Kasar Katsina ta yi suna a kan irin wannan tsari na hawan gadon sarauta. Wasan

kwaikwayon ‘Yanka Masabki Baƙon Sanau’, na East (1936:69-80), babban misali ne na wannan kokuwa domin hawa karagar mulki a masarautar Katsina. Za a iya ganin wannan hali na jaruntaka, musamman a kirarin Sarkin Kabi, Muhammadu Kanta, domin ya yi zamani lokacin da aka yi yaƙe-yaƙe a Kasar Hausa, kamar yadda tarihi ya nuna, Kanta jarumi ne cikin jarumai. Kasar Kabi ta taɓa zama ƙarƙashin mulkin Songhai, amma zamanin Sarki Kanta, ƙasar ta yi ƙarfi ƙwarai da gaske, har ta yi wa Askiya tawaye, ta ɓalle, ta sami ‘yancin kanta. Wannan ya sa saboda shahara ko bajintar Kabi, har ƙasar Barno ta taɓa kai mata hari, amma ba ta ci nasara ba. Haka kuma, ƙasar Kabi ce ƙasa cikin Kasar Hausa da masu jihadi ba su ci galaba a kanta ba, wanda ya sa har yau, zuri’a ɗaya ke mulkinta. Jaruntar Sarki Muhammadu Kanta ta fito sarari a kirarin da Zabiyar Kabin Argungu ta yi masa, musamman yaƙinsa da garuruwan Fulani, kamar yadda take cewa:

*Oooh shaɗi,!*

*Arnan bagudu….*

*Yau duniyag ga ba ta rago ta ba Kanta,*

*Haka lahira ba ta rago ta ba Kanta….*

*Ragasa tunku watarma son yaƙi…*

*Mai uba ka sausawa ga ranar yaƙi,*

*Ingarma anka ji anka ba ku Kanta domin yaƙi,*

*Kowwag gane ka ya ga yaƙi,*

*Wanda bai ganka ba bai ga mutuwa ba,*

*Guguwa sha da gatari,*

*Zangon farin wata arewa Kanta.(Kirarin Sarkin Kabi, Muhammadu Kanta).*

Wannan kirari, na Sarki Muhammadu Kanta, shi ake yi wa duk wanda yake sarauta a masarautar Kabin Argungu, ba domin komai ba, sai saboda a tunatar da shi, gidansu, gidan jarumai ne, saboda haka, ya yi gadon jaruntaka daga kaka da kakanni, shi ma kada ya zama mai wargi. A kirarin, mun ga yadda Zabiyar Kabi ke yabon Sarki Kanta saboda jaruntakarsa wajen yaƙi. Ta jaddada cewa Kanta ba rago ba ne a kirarin nata, domin a kullum shirye yake idan dai maganar yaƙi ce. Ba ya tsoro, ba ya fargaba, gama ba a kai masa yaƙi, sai dai shi ya kai, kuma duk wanda ya yi artabu da shi a fagen fama, sai dai buzunsa. Ta kuma siffanta shi da yaƙi saboda jaruntakarsa.

### 5.4 Kyauta

A rayuwa, babu mai son marowaci, ballantana maroƙi, Bello (1976:28). Wannan ya sa tun da ‘kyauta’ ita ce babban abin da maigida zai yi wa maroƙi, ya zama dole, shi kuma maroƙi ya yabi ubangidansa da ita. Makaɗa, musamman na fada, suna yaba kyautar da iyayen gidansu suka yi masu, ta hanyar yawaita godiya, wanda hakan kan sa iyayen gidansu su ji daɗi, su ƙara kyautar da suke masu, ko domin jama’a su ji, abokanan hamayya kuma jikinsu ya yi sanyi, su tsorata. Kafin Hausa (1997), ya bayyana cewa, Sarakuna, kamar kowane irin dan Adam, mutane ne masu

sha'awar nishadi da son girmamawa da kambamawa, domin haka, sukan ji daɗi idan an yi masu kirari, kuma kamar yadda dan tauri ko ɗan dambe kan fito fili ya nuna jin daɗi idan an kambama shi, yadda zai karya wuƙa, ko ya murƙushe wanda ya fi ƙarfinsa, to, haka Sarki yakan nuna ya harzuƙa idan kirari ya shige shi, ta hanyar yin gagarumar kyauta. Za a iya cewa, Zabiyoyin Fada suna ƙoƙari wajen yaba kyautar da aka yi masu, watau ba su kasance butulu ba. Alalmisali, Zabiyar Kabin Argungu a kirarin Sarki Sama tana cewa:

*Da arzikinka ɗan Yaƙuba Nabame,*

*Dukiya ta isa kaya sun isa…(*Kirarin Sarki Sama).

Wannan na nuni da cewa, zamanin Sarki Sama, arziki ya wadaci kowa a masarautarsa, musamman ma, ƙila rukunin mai matanin (makaɗan fada). Idan aka ce arziki ya wadaci jama'ar wani basarake, ko dai saboda hannunsa a buɗe yake, ko kuma a ce iya gudanar da mulki ya sa jama'a suka sami walwala, kowa ya tashi tsaye ya nemi na kansa, saboda kwanciyar hankali, wanda ya yi sanadiyyar wadata da walwala. Kyauta na ɗaya daga cikin ɗabi'un da ke kyautata zamantakewa. A iya cewa Zabiyar Kano ta yaba kyautar Sarkin Kano, Ado Bayero matuƙa, domin godiya ce ta mamaye kirarin da ta yi masa, saboda hannun baiwa, na basaraken. Kamar yadda take cewa:

*Ina godiya Lamiɗo ka bi ya ni,*

*Goyon Malam Maje ka biya ni,*

*Kyauta ba biyan bashi ba…*

*Ina godiya ina ƙarawa na gode…*

*Kun biya ni na gode,*

*Ina godiya ina ƙarawa na gode,*

*Kuma na yi bege mai tada rai,*

*Allah ji ƙan Sarkin Karaye Ibrahim…*

*Ranar sunan Hadiza rannan riga da doki,*

*An biya ni ba bashi ba,…*

*Sarki da hakiman Kano na gode,*

*Autan Bawo Mai Ila ka biya ni na gode ma,*

*Ina godiya ina ƙarawa 'yan Fulani sun biya ni,*

*Kyauta ba biyan bashi ba,*

*Riguna da riguna na gode,*

*Turmi da turame,*

*Ba na dakan gumba ba…*

*Irin Yusufa Nadabo ka biya ni,*

*Ka biya ni na gode ma,*

*Ina godiya ina ƙarawa na gode…*

*Na yi godiya na gode jikan Yaji…(*Kirarin Sarkin Kano Ado).

**5.5 Iya Mulki**

'Iko ko sarauta', ko kuma 'gudanar da harkokin hukuma kan jama'a' shi ne 'mulki'. Idan aka ɗauki ma'ana ta biyu, za mu iya cewa, 'gudanar da harkokin hukuma kan jama'a', shi ne ya fi dacewa da 'mulki'. Watau dammar da shugaba yake da ita ta umarni da hani, ba tare da son kai ba. Wannan ya sa ake son shugaba mai haƙuri, da gaskiya, kuma adali, mai son jama'arsa, da tausaya masu, a kowane hali.Ko zamantakewa ta yau da kullum, a kan so mutum mai gaskiya da haƙuri da adalci, musamman ma aka ce wannan mutum jagora ne na jama'a. Wannan ya sa Hausawa ke karin magana kan waɗannan kyawawan ɗabi'u a kodayaushe, domin tausasa zuciya.Zabiyar Kabin Argungu, a kirarin Sarki Sama, ta siffanita shi da gaskiya, kamar yadda take cewa:

Na Bawa hankalinka gare ka,

*Sama Kowwag ƙi gaskiya ka ƙi shi,*

*Yawan magana kan sa ƙarya,*

*Ai ko kurum magana ta,*

*Jigon Sarakuna ɗan Muhammadu Kanta,*

*Sadaukin Sarakuna na Zarmakwai mai danda,*

*Mulkinka ya wuce 'yar boda…(Kirarin Sarki Sama).*

Ke nan, kamar yadda Zabiyar Kabin Argungu take faɗi a kirarin, Sarki Sama mai gaskiya ne. Mai gaskiya kuwa shi ke iya riƙon amana. Kamar yadda ta ce, gaskiyar basaraken ta sa bai cika magana ba, domin yawan magana kan sa a yi ƙarya. A maimakon magana, a zamanin Sarki Sama, sai dai a gani a aikace, wajen gudanar da mulki da duk abin da ya dace a yi ko a bari, ko kuwa a ce, a duk abin da ya sa gaba, sai ya ga bayansa. Ke nan, yana da dattako, domin babba ba ya magana biyu. Ta kuma kira shi 'jigo/sadaukin Sarakuna', duk dai, saboda bajintarsa da ƙwarewarsa wajen iya riƙe jama'arsa. Da ta ci gaba kuma, ta suranta basaraken da 'mai natsuwa', wato wanda yake cikin hankalinsa a kodayaushe, yake kuma zurfin tunani kafin ya aikata wani abu. Wannan na tabbatar da ƙwarewar Sarakunan Kabin Argungu wajen iya mulki, kamar yadda ta ce a kirarin Sarki Kanta:

*Zullufi –wullufi yawanin alaihin…(Kirarin Sarki Kanta).*

Wato,'taushi da tausasawa'. Ke nan, Sarki Kanta mai taushin hali ne kuma mai tausasawa. Wannan na nuni da halin basaraken na tausayi kuma mai aiki da tausayi, duk kuwa da cewa an san halinsa na nuna jaruntaka a fagen fama, wanda ke cire tausayi a zukatun jarumai, to amma, a tsakaninsa da jama'arsa, mutum ne mai taushin hali da tausaya masu matuƙa.

Haka kuma, sha'anin mulki ana son shugaba mai haƙuri, saboda haƙuri na ɗaya daga cikin muhimman sinadaran cim ma rayuwa, waɗanda suke kai mutum ga nasara, musamman haƙurin babba ga waɗanda suke ƙarƙashinsa. Wannan ya sa Bahaushe kan ce, "Babba juji ne". Zabiyar Daura, ta suranta Sarkin Daura, da haƙuri, kamar yadda take cewa:

*Zabiya : Dosono,*

*`Yan Amshi: Dosono,*

*Zabiya : Ai ya fi kyau,*

*`Yan Amshi : Aiya fi kyau,*

*Zabiya: Sannu ta fi kus…,*

*`Yan Amshi : Sannuta fi kus.(Kirarin Sarkin Daura).*

Kalmar 'dosono', tsohuwar kalmar Hausa ce da take nufin 'mai haƙuri'. Zabiyar ta nuna muhimmancin yin haƙuri, musamman ga shugaba. Kirarin ya jaddada cewa, yin haƙuri ya fi rashinsa, domin kuwa "sannu ta fi kusa", kamar yadda ta faɗi a cikin kirarin. Ke nan, duk wanda ya yi haƙuri, a kwana a tashi zai cim ma burinsa.

Ita ma Zabiyar Haɗeja, a kirarin Tafidan Haɗeja da Jarman Haɗeja tana cewa:

*Rumfa sha shirgi,*

*Kwano ba ka karaya….(*Kirarin Tafidan Haɗeja).

Wannan na nuni da haƙurin sarakin, kamar yadda rumfa take, komai aka kwaso, aka jajiɓo, ake ɗora mata a sama. Ta kuma suranta su da 'kwano', wanda ta ce, ba ya karaya. Watau, ba kamar tukunyar ƙasa ba, wadda ƙwarinta bai kai na kwano ba. Wannan, na ƙara nuni da cewa, a mulki ba a son basarake mai nuna karaya, sai gwarzo, gawurtacce domin ya ba jama'arsa ƙarfin gwiwa, na iya riƙe su da sama masu kariya, musamman lokacin da ake yaƙe –yaƙe.

**6.0 Kammalawa**

Babu shakka, daga bayanin da aka gani a wannan muƙala, Zabiyoyin Fada sun bi sawun 'yan'uwasu maroƙa wajen ƙoƙarin yabon saraki da shikashikan cim ma yabo.Makaɗan fada suna amfani da yabo a duk waƙoƙinsu da kirari, domin sun ɗauki yabo kamar shi ne wuƙa shi ne nama, domin babu abin da fi faranta ran saraki kamar a yabe shi da asalinsa ga sarautar gidansu, da jaruntakarsa da ta iyaye, da kyauta,da iya riƙon jama'arsa, da kuma riƙe addini da tabbatar da shi. Idan kuwa akayabi mutum, ana faɗin abubuwa na gari a kansa, domin a girmama shi. A wani gefe kuma ya ƙara masa farinjini a idanun jama'a, sannan kuma a razana abokanan hamayya.

## Manazarta

Abrahams, R.C. (1967). *Dictionary of the Hausa Language*, Second, London: University of London Press Limited.

Bargery, G.P. (1993). *A Hausa English Dictionary and English Hausa Vocabulary (*2nd ed) Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Bello, G. (1976). "Yabo, Zuga da Zambo a Waƙoƙin Sarauta", Cikin *HarsunanNijeriya* (iv) CSNL, Kano: Abdullahi Bayero College, Ahmadu Bello University.

Diso, A. H. (1997). Zambo da Yabo a Matsayin Dabarun Jawo Hankali a Rubutattun Waƙoƙin Siyasa, Kundin Digiri na Tsakiya, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (1988). Waƙoƙin Fada, Sigoginsu da Yanaye – Yanayensu, Musamman a Kasar Sakkwato, Kundin Digiri na Koli, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (2000). "Kirari a Waƙoƙin Makaɗan Hausa", in Hausa Studies, Vol. II, No 12, a Journal of the Department of Nigerian Languages Usmanu Ɗanfodiyo University.

Gusau, S.M. (2008). *Waƙoƙin Baka a Kasar Hausa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu,* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Hauwa, M. (2008). "Karin Harshe na Rukuni a Hausa: Nazari a Kasar Zazzau", Kundin Digiri na Tsakiya, Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Ibrahim, M.S. (1985). "Gudunmuwar Adabin Baka Wajen Raya Al'adun Gargajiya na Hausa", Cikin Rufa'i A da Wasu (ed), *Nazari a kan Harshe da Adabi da Al'adun Hausa*, CSNL, Kano: Jami'ar Bayero.

Ibrahim, M.S. (1988) *Kowa Ya Sha Kiɗa*, Lagos: Longman Publishing Company Limited.

Kafin Hausa, A.U. (1985). Kirari a Hausa: Matsayinsa da Yanayinsa, Kundin Digiri na Tsakiya, Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Kafin Hausa, A.U. (1997). " Kirarin Sarakuna da na Garuruwa", Cikin *HarsunanNigeriya*, xviii CSNL, Kano: Jami'ar Bayero.

Mack, B.B. (2004). *Muslim Women Sing: Hausa Popular Song*, Bloomington and Indianapolis: Indiana University Press.

Mazawaje, M. I. (1985), Zambo da Habaici a Waƙar Fada, Kundin Digiri na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Tsoho, M.Y. (2001). Tubalin Ginin Yabo: Tsokaci Kan Yabau a Waƙoƙin Iko, *FAIS Journal of Humanities* Vol.1, No.4, Kano: Bayero University.

Tsoho, M. Y. (2002). Elogues, the Building Blocks of Hausa Praise Song: A Thematic and Structural Examination, Unpublished PhD Dissertation, Department of Nigerian and African Languages, Zaria: Ahmadu Bello University.